# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Aljannar Kare – Haɗarin afkawa cikin bashi
## Kashi na biyar: Haɗarin fuskantar asara

| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | James Muhando |
| Wanda ya fassara: | Danlami Bala Gwammaja |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Mai ba da labari: | ɗan shekara 30 |
| Lawan: | ɗan shekara 40 |
| Bash: | ɗan shekara 15 |
| 'Yar sanda: | 'yar shekara 35 |
| Yallaɓai: | ɗan shekara 50 |
| Ado: | ɗan shekara 45 |
| Jamila: | 'yar shekara 15 |
| Ali: | ɗan shekara 15 |
| Zaliha: | 'yar shekara 35 |
| Ligidi: | 'yar shekara 35 |
| Ɗan daba na 1: | ɗan shekara 45 |
| Ɗan daba na 2: | ɗan shekara 45 |

**Mai ba da labari:**

Muna yi wa abokan hirarmu barka da saduwa da ku a cikin kashi na biyar daga cikin shrinmu na “Ji Ka Karu” mai suna “Aljannar Kare – Haɗarin Afkawa Cikin Bashi”. Haka kuma muna yi muku barka da zuwa wannan wajen wanka! Ai kun tuna da ni ko? Ni ne Aliyu Bello, abokin hirarku a wannan shirin, ina kuma aiki ne a banki. Na san tunanin da kuke yi: wato gayen nan ya samu kuɗi sai shanawa kawai yake a wajen wanka. Amma ba haka ba ne. Na gaji da kirana Tundurki da mutane suke yi kamar yadda Jamila ta dinga kirana lokacin da muna makaranta! Shi ya sa nake zuwa wajen wanka don na rage ƙiba. Amma a gaskiya duk lokacin da na yi iyo sau ɗaya, sai na ɗan ɗare kan kujerar nan mai lilo na ɗan sarara.

To, amma maimakon bajewar nan da na yi a nan, bari na koma da mu zamanin da kaina yake hayaƙi, ina matashina kuma ana kirana Ali. A wancan kashin na ba ku labarin yadda Kawu Natanko ya ranci kuɗi a wajen Malam Audu, duk da cewa a lokacin ya ci bashi har iya wuya. Wannan shi ne irin kuskuren da muka so mu tabka lokacin da muka kai Bash wajen Malam Ado mai ba da bashi! Bash dai ya ciwo bashin keke wanda hakan ya jefa shi cikin matsala. Lokacin da baban Bash, wato Lawan, ya gano cewa ɗansa ya kwaikwayi sa-hannunsa don a ba shi bashi, kunnensa ya kama har ya fito da shi daga aji. Sai da hankalin Bash ya yi matuƙar tashi yayin da ya gano inda babansa ya nufa da shi.

**Fitowa ta 1: A caji ofis**

| | |
|---|---|
| **Lawan:** | Zo mu je, wawan yaro kawai! |
| **Bash:** | Don Allah Baba, kada ka kai ni wajen ’yan sanda! Na tuba Baba, ba zan ƙara ba! |
| **Lawan:** | Ina! Ai yau za ka girbi abin da ka shuka. Ni ban san ina kiwata mai laifi a cikin gidana ba! |

**Bash:** Kulle ni fa za su yi, Baba!

**Lawan:** Ai, kamata ya yi a ce ka yi tunanin wannan abin tun kafin ka aikata shi! … Zauna! Zauna, ka jira ni. Kada kuma ka kuskura ka ce za ka gudu. Ga ga waccan 'yar sandan? Ka motsa, zan sa ta kama ka. … Yallaɓai! Don Allah ki kula mini da yaron nan kafin in dawo!

**'Yar sanda:** Ba matsala, Alhaji! … Maza, zauna a nan!

**Yallaɓai:** Shigo.

**Lawan:** Ranka ya daɗe, na dawo!

**Yallaɓai:** To ka dawo, Lawan! Ka zo da yaron?

**Lawan:** E, na zo da shi. Kamar dai yadda muka tattauna da farko, ku ɗan tsorata mini shi. Amma don Allah kada ku sa shi a cikin *'cell'* ɗin da kuke sa masu manyan laifuffuka! So dai nake ya gane kurensa.

**Yallaɓai:** Kada ka damu, Lawan. Ka sa shi a hannu na gari. Ka zo ka tafi da shi gobe da safe.

**Lawan:** To, shi ke nan. Allah ya kai mu!

**Mai ba da labari:**
Ta wannan hanya wannan babban aboki nawa ya fara fuskantar fushin hukuma. Amma fa ba hukumar ce ta dame mu ba. Kamata ya yi a ce mun biya Malam Ado kuɗinsa tun tuni, amma ba mu biya ba saboda ba mu da kuɗi. Mu a garinmu ba ma samun kuɗi sai an yi hutun watan Disamba, wato da kaka, zamanin da muke samun 'yan aikace-aikace. Kuɗin da muka ranto a

wajen Malam Ado kuma yana ta ƙaruwa, kuma ga shi mun kasa biya! Mun ma sauya hanyarmu zuwa da dawowa daga makaranta don kada mu haɗu da Malam Ado. To, amma fa shi ba a banza ake kiransa da mai ba da bashi da ruwa ba. Ai sai da ya farauto mu a kan hanyarmu ta zuwa makaranta.

**Fitowa ta 2 : Ado ya kai hari**

| | |
|---|---|
| **Jamila:** | Ya kamata mu biya ta gidan su Bash mu duba shi. |
| **Ali:** | An sako shi daga caji'ofis ne? |
| **Jamila:** | Na faɗa maka Ligidi ya ce an sako shi! |
| **Ali:** | Yaya aka yi Ligidi ya sani? |
| **Jamila:** | Haba Tundurki! Baban Ligidi a caji'ofis yake aiki fa, ko ka manta ne? |
| **Ali:** | Af haka ne fa! Na manta ne! |
| **Jamila:** | Kai Ali, wallahi, maza mu gudu! |
| **Ali:** | Haba Jamila! Kina so ki tsoratar da ni ne? |
| **Jamila:** | Ga Malam Ado nan a bayanka! |
| **Ali:** | Mene ne haka ne! |
| **Jamila:** | Mu gudu! Ali, mu ruga! |
| **Ado:** | Na kama ku, ƙananan ƙwari! Ku biya ni kuɗina! |

**Jamila:** Wayyo, hannuna ya karye!

**Ado:** Yauwa! Na kama ki! Kuna ganin za ku guje mini ne? Kuna jin za ku karɓi kuɗina sannan ku yi mini layar zana ne?

**Jamila:** Ali, don Allah ka taimake ni! Kada ka tafi ka bar ni!

**Ali:** Ka sake ta!

**Ado:** Kuna ganin za ku iya damfarata ne? Zo nan!

**Jamila:** Wayyo hannuna! Ka ji min ciwo fa!

**Mutum na 1:** Kai, me yake faruwa nan ne?

**Ado:** Wata yarinya ce nan, ina jin faɗuwa ta yi ta kuma karye a hannu! Ka san yaran zamani, ba sa ji!

**Mutum na 2:** Tsayar da motar can! Mu kai ta asibiti!

**Ado:** In kika faɗi abin da ya faru sai na kama ki na kashe ki! Kin ji ko?

**Mutum na 1:** Af, ina mutumin nan ya yi kuma?

**Mutum na 2:** Ba Ado ba ne, mai bayar da bashi?

**Ali:** Malam Ado ne! Shi ne ya biyo mu da gudu, ta faɗi ta karye a hannu!

**Mutum na 1:** Shi Malam Ado ya biyo ku? Saboda me?

**Ali:** Abokinmu ne ya ranci wasu kuɗi a wurinsa, kuma bai gama biya ba tukuna.

**Mutum na 2:** Kuka ranci kuɗi a wurin Malam Ado? Ba ku san ko wane ne shi ba?

**Mutum na 1:** Kama ta, mu ɗauke ta.

**Mutum na 2:** Yi a hankali, kula da hannunta! Mu yi sauri mu kai ta asibiti!

**Mutum na 1:** Direba, mu je!

**Mai ba da labari:**
Matsalar wannan bashi da bai taka kara ya karya ba, ba ta tsaya a kan wanda ya ciwo bashi kaɗai ba, wato Bash, abin ya haɗa har da mu abokansa waɗanda ba mu ci ba, ba mu sha ba! Kai har babata Zaliha da ƙawarta Fati sai da aka tsoma su a wannan al'amarin. Bari mu ji yadda ta kasance musu a ranar da ni da Jamila muka guje wa Malam Ado.

**Fitowa ta 3: A kasuwa**

**Ɗan kasuwa na 1:** Ga mu fa da tufafi irin na zamani! A zo a duba! …

**Ɗan kasuwa na 2:** A sai tumatur mai kyau! Ga tumatur mai kyau fa! Yauwa, Hajiya, zo ki duba!

**Fati:** Maigida, ba ni tumaturin nan kilo ɗaya!

**Ɗan kasuwa na 2:** Yauwa Hajiya, kilo ɗaya ko? Madalla. Hajiya, ga shi. Kuɗinki ya kama Dala ɗaya ke nan!

**Fati:** Ga shi, ungo kuɗinka!

**Ɗan kasuwa na 2:** Na gode, Hajiya! Yauwa, sauka lafiya. … A zo a sai tumatur! Ga tumatur mai kyau! …

**Fati:** Zaliha, na ɗauka ke ma za ki sayi tumaturin. Zaliha! Zaliha! Tunanin me kike yi ne?

**Zaliha:** Uhm! Ina jinki, Fati! Me kika ce?

**Fati:** Ina hankalinki ya yi ne? Me ya faru?

**Zaliha:** Ban sani ba ko tsarguwa kawai na yi, amma ina jin waɗancan mutanen kamar binmu suke yi!

**Fati:** Waɗanne mutane?

**Zaliha:** Ga su nan a bayana! Ɗaya ya sa shuɗiyar hula, ɗayan kuma ya sa *'jacket'* ta fata mai ruwan ƙasa-ƙasa. Na lura tun da muka fito daga gida kamar binmu suke yi a baya.

**Fati:** Tsarguwa kawai kika yi! Me zai sa su dinga binmu?

**Zaliha:** Haka nake jin jikina 'yan kwanakin nan. Jikina ne yake ba ni kamar ana sa mini ido.

**Fati:** Ki yi maza ki sayi abin da kike buƙata! Kamata ya yi mu yi sauri mu koma gida, kar dare yi!

**Mai ba da labari:**

Kamata ya yi a ce Fati ta ji maganar da babata ta faɗa mata. Tabbas mutanen

nan binsu suke yi. Ita kanta Fati ɗin, ƙawar Babar tawa, ta haƙiƙance binsu ake yi yayin da suke komawa gida! To su wane ne waɗannan mutanen, kuma me suke nema? A ɗaya ɓangaren kuma a asibiti, Jamila ta farka, hannunta nannaɗe da filasta.

**Fitowa ta 4: A asibiti**

**Ali:** Yaya jikin naki?

**Jamila:** Me kake tsammani? Ciwo na damuwa mana!

**Ali:** Ki yi haƙuri, Jamila! Ba yadda zan yi ne. Ganin Malam Ado ya sa na firgita wanda hakan ya sa na dinga gudu ba ƙaƙƙautawa!

**Jamila:** Shi ne ka gudu ka bar ni a hannun wannan tsohon mai laifin!

**Ali:** Ai ba yadda zan yi ne, Jamila.

**Jamila:** Ai da ka nuna masa kai ma namiji ne, ko da kuwa ihu ka yi don mutane su kawo mini taimako.

**Ali:** Wato dai yanzu kina ganin laifina ne ke nan?

**Jamila:** E, kai na ɗora wa laifi! Sai da na faɗa maka cewa Malam Ado ba shi da mutunci, amma ka yi watsi da maganata! Cewa ka yi abokai ba sa rabuwa, ko ba haka ka ce ba? To, me ya sa ka gudu ka bar ni a hannun Malam Ado?

**Ali:** To, ni dai ba abin da zan ce miki sai dai in ce ki yi haƙuri don Allah, Jamila!

**Jamila:** Je ka kawai!

**Ali:** Haba Jamila, don Allah ki yi haƙuri! *Please!*

**Jamila:** Don Allah tafi, ka ba ni wuri, ba na son ganinka!

**Mai ba da labari:**

Kun dai san ina cikin damuwa, don kuwa akwai alaƙa ta ƙut-da-ƙut tsakanina da Jamila! Ga shi yanzu tana ganin laifina a kan abubuwan da suka faru. Duk sai na ji Bash ya sure min!

A kan hanyata ta zuwa gida sai na dinga addu'ar Allah Ya sa dai babata ba ta ji abin da ya faru ba. Haka na shiga gidanmu mai cike da bishiyoyi. Ga shi dare ya yi. Na kuma ji muryar maza biyu suna magana ƙasa-ƙasa. Sai na laɓe a bayan wata bishiya a tsorarce. Ina tunanin me ya kawo su gidanmu a wannan lokacin? Na kuma tabbatar ba su gan ni ba.

**Fitowa ta 5: A gidan su Ali**

**Ɗan daba na 1:** Ka tabbatar nan ne gidan?

**Ɗan daba na 2:** Ba ka ga san da ta shigo nan ba?

**Ɗan daba na 1:** Ai ba lallai ba ne a ce nan ne gidansu.

**Ɗan daba na 2:** Ba wai cewa na yi nan ne gidansu ba, amma ba mamaki a nan yake ɓuya.

**Ɗan daba na 1:** To yanzu mene ne abin yi?

**Ɗan daba na 2:** Sai mu jira har sai ya dawo.

**Ɗan daba na 1:** Ana wannan sanyin? Kai! Ina! Mu tafi kawai, ma dawo gobe.

**Ɗan daba na 2:** To me za mu ce da *'boss'* idan ya kuɓuce mana ya sake ɓuya? An faɗa mana duk inda muka gan shi, kada mu rabu da shi.

**Ɗan daba na 1:** Ina jin matan nan fa sun gane muna binsu lokacin da suka taho daga kasuwa!

**Ɗan daba na 2:** Wannan ne ma zai sa mu tsaya don kada su faɗa masa ya gudu!

**Mai ba da labari:**
To, da wannan labari mai ban tsoro na ƙuruciyata muka kawo ƙarshen wannan wasan na yau. Ku tara a gaba don jin ko su wane ne waɗannan masu laifi, me kuma suke nema? Kuma shin ko mun warware dukkan matsalolinmu? Idan kuna son tuntuɓata sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kuna kuma iya saduwa da mu a shafinmu na 'Facebook'. To yanzu kuma bari na ɗan yi iyo ko na samu na rage girman tumbina. Sai an jima, ku huta lafiya!